# Dokokin Duniya Kan Hakkin Bil'adama, Na Majalisar Dunkin Duniya

In commemoration of the *Fiftieth Anniversary of the Universal Declaration of Human Rights (1948-1998)*

# Dokokin Duniya Kan Hakkin Bil'adama, Na Majalisar Dunkin Duniya

# Dokokin Duniya Kan Hakkin Bil'adama, Na Majalisar Dunkin Duniya

A TRANSLATION OF THE
UNIVERSAL DECLARATION
OF HUMAN RIGHTS

*Into*

# HAUSA

# DOKOKIN DUNIYA KAN HAKKIN BILADAMA, NA MAJALISAR DUNKIN DUNIYA

A 10 ga watan Disambar shekara 1948 ce babban Zauren majalisar ɗunkin duniya ya amince da waɗannan dokokin kan haƙƙin bil'adama, domin haka ne har zauren ya kirayi duk ƙasashen da ke cikin majilisar ɗunkin duniya da su rubuta wannan dokokin kuma su watsa su cikin makarantu da cibiyoyin ilimi a cikin kesashensu, ba tare da nunin bambancin ƙungiyar siyasa, ko na kasa, ko muhalli ba.

Yanci, da adalci, da zaman lafiya ba zasu sami girkuwa ba duniya sai Idan an amince da mutuncin bil'adama, baiwa bil'adama hakkin bai ɗaya a ɗuniya tukuna.

Rena ɦaƙƙin bil'adama ko keta alfarmar su yana haifar da munanan halaye da duniya baki ɗaya ke fushi da shi, haka kuma samar da al'umar da cikinta ake samun 'yancin furuci, 'yancin addini, da kubuta daga kowanne irin tsoro shine gurin koli a wurin talaka.

Domin kawar da tawaye da mulkin danniya shi yasa aka kafa dokokin da zasu ƙwato wa duk wanda aka zalunta hakkinsa, bunƙasa ci gaban lumana da abokantaka tsakanin ƙasashe abu ne mai Muhimmanci,

Mutanem da ke cikin Majalisar ɗunkin duniya sun jaddada imaninsu akan 'yancin bil'adama a cikin tsarin mulkin majalisar,har ila yau sun ce mutunci da kimar bil'adama, kai ɦada da daidaita jinsinmaza da mata yana da Muhimmancin gaske, haka sun ce bunkasa ci gaban jama'a da samar da rayuwa kyakkyawa na cikin ƙudurinsu.

Haka nan ƙasashen da ke cikin majalisar dunkin duniya, tare da hadin guiwar majalisar sun ɗauki alkawarin zasu bunkasa a duniya abin da zai sa a kiyaye hakkokin bil'adama da duk abin da yake hakkinsu ne.
Fahimtar hakkokin bil'adama da duk abinda yake 'yancinsu ne yana da Muhimmanci ga cimma kudurin majalisar ɗunkin duniya. domin haka;

## BABBAN ZAUREN MAJALISAR DUNKIN DUNIYA YA AMINCE DACEMA;

Abubuwan da wannan dokokin 'yancin bil'adama ya kunsa ya zamanto gurin da duk al'ummu da ƙasashen duniya suke da manufa ɗaya akan sa kuma suke fatar cimma, kasancewar wannan gurin da shi suke kwana suna tashi zasu kokarta wajen karantar da jama'a da waye musu kai domin biyayya ga wadannan hakkokin da 'yancin' haka nan kuma zasu yi amfani da ra'ayin mazan jiya wajen ganin ta aiwatar da wannan dokokin, wannan kuwa zai kasance ne ga duk ƙasashen da ke cikin majalisar dunkin duniya da waɗanda ke ƙarkashin mulkinsu.

## DOKA TA 1

Duk ɗa n'adama ana haihuwar **su ne** 'ya'ya 'Yantattu, kuma Mutuncinsu **da** hakkokinsu dai-dai yake da na **kowa, domin** suna da tunani da cikakken hankali, **sabo - da** haka ake son duk mu'amalar da za'a yi **tsakanin** bil'adama ta kasance akwai 'Yan'uwantaka tsakani.

## DOKA TA 2

Kowa na da damar cin moriyar **da** waɗannan dokokin 'yancin bil'adama ya shinfida, ba tare danuna kowanne **irin** banbamci ba, kamar banbamcin ƙabila, Launi, jinsi, harshe, addini, siyasa ko dai wani **ra'ayi** da keda alaƙa da ƙasa, al'adar wuri, **talauchi, haihuwa** ko dai wani matsayi.

Har ila yau babu wani banbamci **da za'a** nuna wa mutun da ya shafi siyasa, **ko shara'a,** ko dai wani matsayi da ya shafi cikin **gida ko** waje. Wannan ƙasar mai 'yanci ce **ko mara** 'yanyci.

## DOKA TA 3

Duk, mutun nada hakkin rayuwa, cikakken 'yanci da tsaron dukiya ko rayuwarsa.

## DOKA TA 4

An hana bauta da bautarwa, kuma saye ko sayar da bayi haramtacciyar sana'a ce.

## DOKA TA 5

Babu wanda za'a yiwa ƙeta ko a azabtar da shi ba tare da hakke ba, haka nan kautar da bil'adama ko wahal da shi ya zama haramiya.

## DOKA TA 6

Doka ta baiwa kowa daman cin moriyar zaman sa mutun duk'mda ya samu kansa.

## DOKA TA 7

Ga doka babu banbamci tsakanin sarki da talaka domin haka suna da kariya iri ɗaya na shara'a, haka nan kuma kowa na da kariyar shara'a akan wani nau'in banbamci wanda ya saɓawa wannan dokokin.

## DOKA TA 8

Kowanne mutun Idan yaga za'a aikata abin da zai hana shi hakkokinsa ko 'yancinsa, da tsarin mulki ko dokar ƙasa ta tanada masa, yana da damar kai kara agaban kotun musamman da kasarsa ta tanada domin yin hakan.

## DOKA KA 9

Babu wanda za'a tsare, ko a ɗaure, ko a sanya shi gudun hijira ba gaira ba sabar.

## DOKA KA 10

Hakkin mutun ne a daidaita shi da kowa a wajen zaman kotu, domin tabbatar da shara'a mai adalci, Inda mutane ke iya zuwa su saurara na tabbatar da hakkinsa ne ko kuma domin a tuhumce shi da wani laifi da ya yi.

## DOKA TA 11

a. Duk wanda aka tuhuma da wani laifi, kuma aka kai shi kotu to yana nan

matsayin mara laifi, sai bayan kotu ta yi rinyaje akansa tare da bashi daman kare kansa ya kasa a cikin zaman kotun da jama'a ke zuwa saurare, sannan ya tabbata mai laifi.

b. Babu wanda za'a ɗaure domin ya aikata kuskure ko laifin da dokar ƙasa ko ta duniya bata amince da zaman sa laifi ba a lokacin da aka aikata shi, koda kuwa daga baya ya zamo laifi. Haka nan ba za'a yiwa mutun hukunci fiye da irin abin da doka ta tanada ba a lokacin da aka yi wannan laifin.

## DOKA TA 12

Babu wanda za'a yiwa katsalandan ko leƙen asirin abin da ya shafe shi, ko iyalinsa, ko gidansa, ko kuma wasikunsa, haka ba za'a keta alfarmarsa ko mutuncinsa ba, kowa na da kariyar shara'a akan ireiren Irin waɗannan shisshigin.

## DOKA TA 13

a. Kowanne mutun na da 'yancin kai-da-komowa, haka nan yana da cikakken daman zama cikin jihar da yake so.

b. Mutun na da 'yancin barin ƙasarsa ya je wata kasa, haka yana iya dawowa duk lokacin da yake bukata.

## DOKA TA 14

a. Idan ana tsangwamar mutun a kasarsa domin siyasa, yana da 'yancin neman mafakar siyasa a duk ƙasar da ya ke so.

b. Wannan 'yancin ba zai hana a tuhunci mutun ba Idan har an tabbatar da cewa ya yi munan an laifin siyasa ko wani laifi da ya sabawa dokokin majalisar dunkin duniya.

## DOKA TA 15

a. Kowanne mutun na da 'yancin zama ɗan wata ƙasa.

b. Babu wanda za'a tuɓewa rigarsa ta zama ɗanƙasa ba tare da ƙwakƙwaran dalili ba, haka ba za'a hana masa ɗaman canza ƙasa ba Idan ya ga dama.

## DOKA TA 16

a. Maza da matan da suka Isa aure suna da daman auren duk wanda suke so kuma su hayayyafa ba tare ba banbamcin launin fata ba, ko banbamci ƙasa, ko addini ba. Suna da cikakkan 'yancin wurin sha'anin aure, da kuma wurin rabuwa.

b. Ba za'a ɗaura aure ba sai da yardar ma'auratan biyu (Namji da mace).

c. I yali ne tushen samar da al'uma, domin haka dole ne al'uma da kasa su yi tanadin dokokin da ke kare iyali.

## DOKA TA 17

a. Kowa na da 'yancin mallakar dukiya shi kadai ko kuma ta hadin guiwa.

b. Babu wanda za'a ƙwace wa dukiya ba tare da hakki ba.

## DOKA TA 18

Kowanne mutun na da 'yancin yin tunanin kansa, 'yancin bin addinin da ya ke so, ko ra 'ayin da ya bada gaskiya da shi, haka yana da 'yancin sake addini ko ra'ayin da ya bada gaskiya da shi, shi ɗaya, ko cikin taro, a ɓoye ko a bayyane, ta hanyar koyarwa ko yin abubuwan da abin da yake bautar ya umurce shi da yi.

## DOKA TA 19

Kowanne mutun na da 'yancin riƙe ko faɗan ra'ayinsa, wannan 'yancin kuwa ya ƙunshi hana yin shisshigi ga duk wani ra'ayin mai ra'ayi, tare da bashi daman yaɗa ra'ayin. Sa a gidajen jaridu ba tare da nunin banbamci gare shi ba.

## DOKA TA 20

a. Kowa na da 'yancin yin taron da bana tada hankali ba da na jamiya.

b. Babu wanda za'a tilastawa shiga wata ƙungiya.

## DOKA TA 21

a. Kowanne mutun na da 'yancin taka rawa cikin mulkin ƙasarsa da kansa ko kuma ta hanyar wani wakili da ya zaɓa.

b. Duk dankasa na da 'yancin yin duk irin aikin da ya ke so a ƙasarsa.

c. Yadda duk ra'ayin mutanen kasa yake haka nan za'a gudanar da mulkin kasar, sannan masu mulkin za'a zaɓe su ne ta hanyar jefa ƙuri'a wanda babu cuta a cikin sa.

## DOKA TA 22

Mutun a matsayinsa na daya daga cikin halittun da suka gina al'umma, yana da 'yancin jin dadin rayuwarsa cikin kwanciyar hankali da tsaro kyakkyawa, kuma zai morewa wannan jindadin ne da hadin kan ƙasarsa da sauran kasashen duniya dai-dai da ƙarfin tattalin arzikin kasarsa, haka tattalin arziki, da jin dadin jama'a, da al'adu na cikin abubuwan da zasu tabbatar da mutuncin sa da bashi daman

gina kansa domin zama muhimmin mutun a cikin al'uma.

## DOKA TA 23

a. Duk mutun na da 'yancin zaɓen duk irin aikin da ransa ke ra'ayi, kuma doka zata kare shi wurin aikin da kuma kariyar rashin aikin yi.

b. A wurin aiki iri daya za'a yiwa kowa jingan bai-ɗaya (wani baya finwani).

c. Duk ma'aikaci zai samu albashi mai tsoka, wanda zai taimaka masa shi da iyalansa su rayu, (rayuwa irin ta bil'adama.) Kuma za'a kare shi da iyalansa daga duk wata matsalar rayuwa.

d. Kowa na da 'yancin kafawa ko shiga ƙungiyar ƙwadago da ransa ke so, domin kariyar ra'ayinsa.

## DOKA TA 24

Kowa na da 'yancin samun lokacin da zai huta, haka nan a ƙalla zai tafi hutu sau ɗaya a cikin shekara tare da albashinsa.

## DOKA TA 25

a. Kowa na da Ikon samun kyakkyawan abinci, sutura, makwanci, kayan kula da lafiya kayan morewa rayuwa, kriyar rayuwa da aiki, kariya daga cuta, tawaya kai duk abin da yake cuta wa bil'adama za'a yi kokarin kare shi da iyalansa gare ta.

b. Mata da yara suna da wata kariya ta musamman, yaran kuwa wadanda aka haifa ne cikin aure ko kafin auren.

## DOKA TA 26

a. Duk yara na da hakkin a basu ilimi kyakkyawa. Za'a bada ilimi kyauta akalla a makarantar firamare kuma ya kasance dole ne ga kowa. Ilimin fasaha da na koyon sana'a kai hadda na jami'a ana son ya kasance kofofinsu bude suke ga kowa muddin dai an cika kaidojin samun su.

b. Dole ne manufar ilimi ya kasance abin da zai samarwa bil'adama jin dadin rayuwa, da karfafa kiyaye hakkokin sa da 'yincinsa,

har ila yau ilimi abu ne da zai taimaka wajen bunkasa fahimtar juna, da ragowa tsakanin jama'a kome saɓnin launin fatarsu da addininsu. Kuma ilimi zai taimakawa majalisar dunkin duniya wajen tabbatar da zaman lafiya a duniya.

c. Mahaifa keda hakkin zaɓawa yaransu irin ilimin da za'a karantar da su.

## DOKA TA 27

a. Kowanne mutun na da 'yancin bada gwargwadon gudunmuwarsa ga duk al'adun al'umarsa, da cin moriyar abubuwn da ake kagowa domin nashadi. Haka yana da damar taimakawa ga ci gaban kimiyya da fasaha, ko kuma yin amfani da sakamakon binciken kimiyya da fasahar da al'umarsa ta gano.

b. Kowa na da hakkin kariyar kyawawan dabiu da wasu Muhimman lamurra domin cin moriyar abin da ya ƙirkiro a fannin kimiyya, hikima ko ɗabi'a

## DOKA TA 28

Nauyin kowa ne na ganin an sami doka ta cikin gida da waje domin tabbacin cewa wadannan dokokin hakkin bil'adama da majalisar dunkin duniya ta tsara sun sami zama a duniya Sosai.

## DOKA TA 29

a. Nauyin mutun ne bautawa al'umarsa da ya ke rayuwa a cikinta, domin a cikin ta ne yake samun karfafa darajarsa ta bil'adama cikin yanci.

b. Wurin morewar 'yanci da hakkokin mutun ba'a. son. mutun ya wuce iyaka, domin haka ana son mutun ya kiyaye zaman jama'a da jin dadin rayuwarsu, kamar dai yadda aka sani a cikin al'umar da ke aiwatar sa dimukuradiyya.

c. Ba wata dama da aka baiwa mutun ta yin amfani da 'yanci da hakkokin nan da majalisar dunkin duniya ta yi tanadi a akasi (ba ta hanyar da aka yarda ba).

# DOKA TA 30

Ba wata doka a cikin waɗannan dokokin wadda wata ƙasa, ko wani mutun, ko wata ƙungiya zata yi ikirari da shi cewa ya bada daman rushe waɗannan dokokin da majalisar dunkin duniya ta yi tanadi.

We acknowledge with thanks the translation into Hausa by Mallam Garba Yinusa

Produced by The United Nations Information Centre (UNIC)
Tel: 2694886
Printed by **donald rowlands** LTD. Tel: 4973953, 7745169.